# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Yesu Babba Mallami



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Byron Unger; Lazarus Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: E. Frischbutter; Sarah S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**

**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**



Yesu babba mallami ne – mafi duka sauran da aka taba yi. Taron jama’a sun saurare shi. Yesu ya gaya musu su zama masu tausayi, da kirki, da hankali. Wadansu za su iya tsanansu ko bata musu rai, amma Allah zai lura da su.



Yesu ya koyar da abubuwa masu yawa. Ya ce mutanen Allah suna haskaka duniya kamar yadda kyendir yake haskaka gida. Ina kwatanci misalin hasken da kyendir zai haskaka daki mai duhu!

**Mutanen da Yesu ya yi magana da su, mutane ne wadanda sun ba da gaskiya ga ramako, "Ido a maimakon ido, hakori a maimakon hakori." Amma Yesu ya koyar da yin kirki, yafewa da kauna, har ga abokan gaba.**



A zamanin Yesu, akwai wadansu da suke rayuwa kamar su masu tsarki ne. Idan sun ba da kudi ga maroka, suna da wani wanda zai hura kaho don kowa ya kalle indaa suke. “Ku ba da kyauta a asirce, Allah kuma zai ba ku lada,” Yesu ya ce.



**Haka ma Yesu ya koyar game da addu'a. Wadansu sun yi addu'a a titi don kowa ya gansu ya kuma ji su. Ba su damu da Allah ba. Su dai sun damu da abinda wadansu suna tunani game da su ne. Yesu ya kira su munafukai – masu aikata karya.**



**Kowane lokaci Yesu ya yi amfani da halitta ne domin ya bayana Koyarwarsa. Misali, ya yi magana game da tsuntsaye. “Ubanku na sama yana ciyar da su,” ya ce. “Kada ku damu. Allah kuma zai ciyar da ku.”**



“Ko ma Solomon a cikin arzikinsa ba a yi masa sutura kamar furen lili ba,” Yesu ya ci gaba da magana. “Idan Allah yana ba da sutura ga ciyawan filaye, ashe ba zai ba ku sutura ba?” Yesu yana koya wa mutane su amince da Allah wanda yake tanada mana duka bukatunmu.



**“Idan ka yi wa dan’uwanka shari’a, ya zama kamar kana kokari ka cire’yar kurar katako ne a idonsa amma kai kana da katon gungumen itace a idonka,” Yesu ya ce. Watakila mutane sun gaggara hadiye miyau. Amma dole su yi tunani a kan ma’anar wannan magana.**





Yesu ya ce mutane su nemi taimakon Allah. Ko iyaye na duniya suna ba da duwatsu ga ‘ya’yansu sa’ad da suka roka burodi? A’a! Sukan ba da abububuwa masu kyau. Allah shi ma yana ba da abububuwa masu kyau ga wadanda suka roka.

Yesu, babba mallami, ya ja mana kunne game da mallaman karya. “Suna sutura kamar tumaki,” Yesu ya ce. “Amma a ciki ciki su kamar kerkeci ne.” Ya ce mallaman karya za a san su bisa ga irin rayuwar da suke yi.



A wani labarin da Yesu ya fada, ya nuna cewa mutanen da suke biyayya ga kalmar Allah suna nan kamar mutum da ya gina gidansa a tushin dutse. Sai babbar hadari ta taso. Bayan da ta kare, gidan ya tsaya daram.



**Amma wawa yakan gina gidansa a kan yashi. Sa’ad da hadari ya bubbuga shi, yakan fadi ya rabu saboda tushin gidan babu karfi. Yesu ya ce mutanen da ba sa biyayya ga kalmar Allah su kamar wannan mutum ne.**



**Taron jama’a suka yi mamaki da kalmomin Yesu. Ba su taba jin irin abubuwan nan ba. Yanzu sun sani ba wai a ji kalmar Allah kadai ba. Dole ne su yi biyayya a kansa kowace rana.**



# Yesu Babba Mallami

## Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

## a na samu a

## Matiyu 5-7, Luka 6

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

42

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin**
**Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi.  Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai.  Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu.  Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama.  Idan ka bada gaskiya ga Yesu.  Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe.  Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi.  Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada.  Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka.  Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin.   Yahaya 3:16**